Kashi na 1
Halin
Allah

# Ko Allah Ya Kan |uya?

Darasi na 1

SAURARA WANNAN! MINITI 10

## Da me kake takama?

Iyayen Amina masu arziki ne don haka suka saya mata mota. Sun ce ta za~I wanda ranta ke so, wato jan marsandi. Tana zuwa makaranta da ita a kullum. Abokanta duka suna kishi ainu kuma takan ji da]in yadda 'yan samari suna duban ta.

**Solomon** ma mutum ne da mutane da yawa sun san shi amma ba saboda ku]insa ba. Ana sonsa saboda bajinta a fannin wasanni. Kowane mutum yana cewa zai tafi was an Olympic nan gaba saboda ya iya gudu sosai-har ma fiye da samaren da sun grime shi. Malamai da 'yan ajinsa duka suna girmama shi.

**Emeka** kuwa mai ilimi ne sosai. Ya koyi karatu tun yana }arami, kuma darasi mai sauki gare shi, shi ne lissafi. Bai zama wa kowa abin mamaki ba lokacin da ya zo na ]aya a kowane darasi a GCE, kuma shi ke kan gaba a JAMB irin da ba a taba ji ba a tarihin makarantar. Iyayensa suna fariya da shi, don haka sai suka shirya masa liyafa. Yana da shirin zuwa jami'a a kasar waje, za a ba shi cikkaken Skolaship.

Dali~ai nan uku suna da abubuwan da za su yi takama a kai amma sun rasa wani muhimmin abu. Ko ka san abin?

NAZARIN LITTAFI MAI TSARKI MINTI 25

## Ko Allah abokinka ne?

**Karanta Irimiya 9:22-24**

1. Wane abu ne ya fi ku]i ko bajinta a wasa, ko zama mai ilimi fiye da kowa?
2. Wa]anne abubuwa biyu ne Allah ya ce mu yi fariya da su a aya ta 24?
3. Wane abu ka sani game da Allah kuma yaya ka ]auke shi? Za ka ce shi abokinka ne ko shi wani abin mamaki ne da ke nesa da kai? Fa]I dalilai.
4. Wa]anne abubuwa uku ne Allah yake so mu sani game da halinsa (aya 24b)?

**Karanta Amos 4:13**

5. Yi tunani a kan Allah:
   - yi tunani lokacin da ya gyara duwatsu.
   - yi tunani a kan yadda ya yi iska da yadda ya juya haske ya zama duhu. Menene sunansa? Ina ma'anar sunan? A tunanika, don me Allah zai so ya "bayyana tunaninsa ga mutum"?

**Karanta 1 Tarihi 28:9**

6. Wane alkawari ne Allah ya yi wa wa]anda suka neme shi? Wa]anne sharu]a ne ke ga nema da samun Allah?
   Ba da misali lokacin da ka ji kamar Allah ya "~uya". Ina dalilin da ya sa ka ji kamar Allah yana ~oye daga gareka?

A KAN ME AKE MAGANA?

A }arshe darasi ya kamata dali~ai su:

- san cewa Allah Mai Iko Dukka yana bayyana tunaninsa ga masu nemansa.
- gain jin da]I game da neman Allah.
- fara amfani da takardar addu'a a ka]aice da fara nazarin Maganar Allah a kowace rana.

ME NAKE BUKATA?

- Littafi mai tsarki
- Littafin rubutu da biro
- Shirya tambayoyi da wuri domin ayyukan aikatawa

# “Na bayyana musu Kowanene kai”

**Karanta Mika 4:11-12 da Zabura 25:14**

7. Ina dalilin da ya sa wa]anda Mika ya yi musu rubutu sun kasa fahimtar tunanin Allah? Wane gargadi aka yi game da rashin sani da fahimtar shirin Allah domin mutanensa?

8. Wane abu ne dabam aka bayyana a Zabura 25:14 ga “masu tsoronsa”? Ina abin }arfafawa saboda iya gaskata alkawaransa?

**Karanta Yahaya 17:25-25**

9. Wannan wani sashi ne na addu’ar da Yesu ya yi wa dukan masu bi. Wane abu ne Yesu ya bayyana wa almajiransa lokaci da yake duniya?

10. Ta wace hanya wannan fahimta ya kasance “a cikinsu” (aya 26)? Ta yaya mu ma za mu san Allah ta wannan hanya a yau?

**Karanta Ayyukan Manzanni 17:24-28**

11. Ta yaya aka bayyana Allah a aya 24?

12. Wa]anne ayyuka uku ne na Allah a duniya aka bayyana (aya 25-26)? Ina manufan Allah a wa]annan ayyuka (aya 27)? Ta yaya wannan aya ta }arfafa mu don mu “neme” shi?



# Ta yaya zan sami, Sanin Allah?

Arabu cikin }ungiyoyi uku do a tattauna na minti 10. bayan haka a taru domin ku bayyana muhimman abubuwan da kuka tattauna.

**{ungiya ta 1.**

Dubi misalign **Amina:**

1. Ko laifi ne da Amina ta sami babbar kyauta haka daga iyayenta? Fa]I dalilai.
2. Wa]ann hatsarori Amina za ta fuskanta saboda samun mota mai kyau haka?
3. Ta yaya za ka mori Mika 4:11-12 don ya gargadi ta a kan ta sa Allah gaba a rayuwarta?

**{ungiya ta 2.**

Dubi misalign **Solomom:**

1. Don me abokasa da malumansa suna ba wa Solomon girma?
2. Tattauna yadda za a mori fariya a bajintar wasa.
3. Ta yaya za ka mori Ayy. Man. 17:24-28 wajen }arfafa Solomon ya ba da ]aukaka ga Allah saboda nasararsa a wasa?

**{ungiya ta 3.**

Dubi misalign **Emeka:**

1. Ko da za ka so ka zama mai ilimi kamar Emeka? Ina dalili?
2. Wane abu Irimiya 9:23-24 ya fa]a mana game da abubuwa mafi muhimmi a rayuwa?
3. Shirya yadda za ka san Allah sosai kuma ka fahimci shirinsa dominka a makonni masu zuwa.

**Kafin a rufe:**

[auki mintoci kuma ro}on Allah ya koya maku yadda za ku san shi sosai.

## Aikin gida na wannan mako

[auki sabuwar takarda ka mai ita littafin yin addu’ar ka]aice. Rubuta abin da ka gane game da Allah, tambayoyin da ka shieya masa da tunanin da ka yi a sakamakon karatu da addu’a a kowace rana. Karanta ayoyi na biye kana yin nazarinsu. Rubuta a littafin rubutu dukan abubuwan da ka koya game da Allah daga ayoyin.

**Rana ta 1.**
Ishaya 40:1-5

**Rana ta 2.**
Ishaya 40:6-11

**Rana ta 3.**
Ishaya 40:12-14

**Rana ta 4.**
Ishaya 40:15-20

**Rana ta 5.**
Ishaya 40:21-24

**Rana ta 6.**
Ishaya 40:25-26

**Rana ta 7.**
Ishaya 40:27-31.